ruwan xafi a jiki don duk sae na tafasa ruwa na bi ta har gidan mijinta na kona ta ni ma" Hurera dake kitchen ta fito tana dariya tace "A'a ba ayi hka ba Inna, Allah dae ya tsare" inna tace "ae ynxu ma daga gidan ubansu nake, kuma yace anjima da daddare xae xo ya gane ma idonsa" Bude kofar falon aka yi, duk suka juya don ganin wnda xae shigo, inna na ganinsa ta tsuke fuska, ya karaso falon fuskarsa a tamke, Rayyanat tayi saurin gyara rigarta, a fusace yana kallon inna ya soma magana "don me xa ki je ki hada ni da Baffana kan wata bnxa can yar kauye Hajiya," inna ta tabe baki tace "sae dae kae ne bakauye ko uwar ka amma ba yar nn ba," xaro ido yyi yana kallonta, ita ma ta yo waje da ido tace "kwarae kuwa!" Rayyanat da tun shigowarsa falon ta sunkuyar da kanta hawaye ya shiga bin kuncinta, ya huzar da iska ya cije lebe lkci daya idonsa ya kada, ya juya fuuu ya fice daga falon, inna tace "Wawa kawae." Baaba hurera ta sauke ajiyar xuciya tace "Ayi hkuri dae inna" mikewa Rayyanat tayi har lkcn hawaye na bin kuncinta, Inna na ganin hka ta rude ta shiga tambayarta lfya, Rayyanat ta kasa bata amsa, hkn yasa inna ta fashe da kuka tace "yo baki ji nace shine dan kauyen ko uwarsa ba, ni dae na shiga uku da 'ya yan kabiru" lkci daya Rayyanat ta hadiye kukan da take tace "kiyi hkuri inna, ni ba shi yasa nake kuka ba, naga ina ta hada ki da jikokin ki ne" cikin kuka ta karashe mgnr, inna ta hade rae tace "suke dae hadani da ke, kuma Allah ya fi su" Baaba hurera tayi murmushi, Rayyanat ta duka ta dauki sauran furan da take sha ta nufi kitchen.

Da rana nasir ya shigo gidansa, ya nufi dakin pretty ganin bbu kowa falon ga ko ina kaca kaca, xaune ya sameta sae fushi take, yaje kusa da ita ya zauna ya shafi gefen fuskarta yace "nasha gaya miki ki daina fushi baya miki kyau," hararar sa tayi snn taja tsaki tace baka son nayi fushi shine zaka kaini qara gun daddy," Nasir ya xaro ido yace "au kin dauka nine, to inna ce taje da kanta ta gaya mai aikin da kikayi don haka ko yanzu kika sake gigin aikata wani abu akan Rayyanat zata je ta snr dashi ne," cike da bacin rae ta tashi tana masa mugun kallo tace"ni yanzu banda lokacin wnn er qauyen bare na qara kulata" ta ja dogon tsaki daga haka ta wuce fuuu! ta barshi nn zaune" girgiza kansa kawai yayi ya tashi yaje ya bud'e fridge ya tsiyaya ruwa a cup yasha.

Washe gari ya gama shirin sa tsaf yaje d'akin pretty wacce yanzu ne tashinta zata shiga Bathroom dmn yin wanka.

Bai qarasa inda take ba a iya gun dressing mirror ya tsaya ya ajiye mata kud'i yace "zanyi tafiya ne ban kuma san yau ko gobe zan dawo ba" ta hade rae tace "ina zaka tafi?" Ya daga kafada yace "Kina da sako ne?" daga haka yyi ficewarsa, ta6e baki tayi gami da jan tsaki tace "aikin banxa, kadda Allah yasa ka dawo ma"

Nasir bai zarce ko ina ba sae gidan inna cike da niyyar ya d'auki Rayyanat ya maida ta gun en uwanta. Bbu kowa falon Inna, hkn yasa ya nemi gu ya xauna yana tunanin ynda xae fita da Rayyanat ba tare da sanin Inna ba, Baaba hurera ce ta shigo falon daga kitchen, da mamaki tace "A'a Nasiru yaushe kuma ka shigo" yyi murmushi ya gaisheta ta amsa da fara'a tana tambayarsa ya kwanan pretty, ya amsa da Alhmdllh snn yace "Baaba Rayyanat xa ki kira min amma fa kar ki bari inna tasan da ina gidan nn" tace "to bari in kirata" ba a dau lkci ba ta dawo falon Rayyanat na biye da ita a baya, hijab ne har kasa jikinta yasan inna ce ta sa aka dinko mata, ya kafa mata ido har ta karaso ta xauna kasa kanta a sunkuye ta gaishesa, ya amsa yana murmushi ya tambayeta ta tashi lfya, kai kawae ta gyada masa, bae kuma cewa komae ba har

na kusan minti biyar hkn yasa ta dago kai tana kallonsa da manyan idanuwanta, murmushi ya sakar mata ta dukar da kanta da sauri, ya kira sunanta a nutse ta amsa ba tare da ta kallesa ba, yace "nasan yan uwanki na cikin tashin hnkli Rayyanat, kiyi hkuri ki gaya min ina ne garin ku" Rayyanat tayi kkrin ganin hawaye bae sakko idonta ba a karo na farko ta gaya masa sunan garin a hnkli, ya gyada kai da gamsuwa yace "to ina xa ki pretty ta kade ki da mota?" Ta girgixa masa kae da kyar tace "garinmu xan ko ma" yyi shiru snn yace "to da me ya shigo da ke kano? Shiru tayi taki cewa komae hkn yasa yace"kin shirya komawa garin naku gun yan uwanki ynxu?" Gyada masa kai tayi kawae, yyi shiru na wani lkci snn yace "to tashi ki dauko ledan kayan ki, amma kar ki Bari Inna ta ganki" tace "to" snn ta nufi dakin da Inna ta bata tana murmushi a ranta tace "don xan tafi ba yana nufin na bar shi bane, har abada baxan bar shi ba, nemo sa baxae min wahala ba tun da na ga gari."

Billy giro😊
🔮🔮🔮🔮🔮🔮🔮🔮🔮🔮
[2:38PM, 5/2/2017] Billy giro😊: 🔮```BAZANBAR SHI BA!```🔮

```Na Billy giro😊```

22/12/2016

🔮```10```🔮

A sanyaye Rayyanat ta dawo falon rike da ledan kayanta ta samu har nasir ya fita xuwa gun motarsa, ita kad'ai yake jira taje ta bud'e gambun motar a hnkli xata shiga ta tsaya cak jin murya inna a bayanta tana fad'in "Rayyanah me zan gani hka ina kuma zakije har da leda a hannunki?"

Sake gambun motar tayi ta juya tare da sadda kanta qasa ta ki barin su had'a ido da inna, ba shiri Nasir ya fito daga cikin mota ya tsaya yana d'an kame kame sbd yanda inna ta tsare shi da ido baki bude.

Kmr xata yi kuka tace " kaddai mayadda rayyanah zaka yi baka ko snr dani ba Nasiru"
```

Ya dan sosa keya yace  "Aa inna, dama wae da.." sae kuma yayi shiru. inna ta fashe da kuka tace "dama me nasiru! mayadda ita zakayi d'in knn, na rasa dalilin da yasa aka rainani hka, ynxu da bn fito ba sae dae in nemi yar nn in rasa" ta fashe da wani matsanancin kuka har da dukawa, Nasir yyi murmushi yace "kiyi hkuri Inna, kuskure ne" inna ta dago ta tsuke fuska tana kallonsa tace "rufe min baki munafuki kawae" dariya yyi yana shafa kansa yace "na yarda, amma inna baki tunanin halin da yan uwanta da iyayenta ke ciki ynxu? Ynxu misali Ikci daya a nemi pretty a rasa wani hali kike tunanin xa mu shiga gaba daya" Ikci daya inba ta marairaice tace "ni fa ban ce kadda a mayar da ita gun iyayenta ba, kawae rashin sanar dani da ba ayi bne ya bata min rae" Nasir yace "to ayi haquri inna,"  ta galla masa harara tace "yo da ban hkura ba da ban tara maka mutan anguwar nn ynxu ba," dariya yyi yana kallonta, tace "ynxu dae dani ya kamata muje gun en uwan nata su ganni nima na gansu na samu ko zasu bar min Rayyanah in rike, ni dae yarinyar ta kwanta min in sonta" ta karashe mgnr cikin kuka, tana matsar kwalla tace "ka ga idan Allah ya kawo mata miji na gari sae tayi auranta,"

Ba yanda nasir ya iya yace "to shiknn inna jeki d'auko mayafinki mu tafi"
Inna ta washe baki ta  ja hannun Rayyanah  tace "zo ki rakani er albarka bazan barki a nn ba don tunda yayi niyya zan iya dawowa na samu ya tafi dake ne kawae,
ko meye dalilin hkn da yyi ne oho," nn dai inna ta jata suka tafi ciki don dauko mayafinta.
Har yaja mota inna bata bar mitan da take ba, hkn yasa nasir sam ya manta da zancen kaiwa umman shi Rayyanat kamar yanda ta buqata.
Tafiya sukayi ba mai wani  nisa sosai ba dmn da kano zuwa qauyensu awa biyu ne sae dai tun lokacin da suka kama hanya Rayyanat keta zubda qwalla a boye har suka isa.
A bakin shiga garin tace da Nasir ya tsaya a nn, ya juya ya kalleta yace "garin naku ba'a shiga da mota ne?" Rayyanat ta daure tace "Ana shiga da ita amma ku sauke ni kawai nagode, zan iya qarasawa da kaina," inna ta yo waje da ido tace "yo Rayyanah ai ni en uwan naki nake son gani ko zan samu sumin alfarmar bar min ke"
Shiru Rayyanat tayi hawaye suka shiga silalowa a hnkli kan kumatunta ta, inna ta saki baki tana kallonta, can tace "Rayyanah ko ba kya son komawa gu nane?" da sauri ta girgixa kanta muryarta na rawa tace "inna ni bani da kowa duk sun rasu"
Inna ta rafka salati da karfi ta fashe da kuka tana cewa "wayyo ni Hajara, wayyo ni" Nasir dae yyi shiru yana kallon Rayyanat amma ya kasa yrda da abinda tace, inna ta ci kukanta ta koshi Rayyanat na taya ta kmr a Ikcn aka yi mutuwar, daga karshe tana fyace majina cikin kuka tace "Allah ya rahama masu, wayyo ni rayuwa" Da kyar Nasir ya iya bude baki yace "Allah ya ji Kansu" ba don ya yrda ba gani yake kmr karya tayi masu.
Cikin muryar kuka Inna yace "to nasiru muje muga mai garin nasu dmn haqqi ne akansa yasan Rayyanat zata zauna gun mu ko?" Nasir ya gyada mata kai kawae ya tada motar ya shiga tafiya a hnkli Rayyanah na nuna mai hanya har suka isa qofar mai gari.
Cikin girmawa aka tarbe su mai garin yyi mamakin ganin Rayyanah ya shiga tambayarta daga ina take, nn Nasir ya dan ji dama dama gnin mai garin ya santa, bayan an gama gaggaisawa Nasir ya zayyano abinda ke tafe dasu yana kallon Rayyanah, mai gari bai musa musu ba ya amince da abinda suka buqata ya Dora da cewa suyi kkrin ganin sun riketa amana don marainiya ce sun samu Ibrin rasuwan mahaifinta, Inna tace "ka ji ka da wata mgna, kasan wacece ni kuwa," mikewa tayi tana washe baki tana kallon Rayyanat tace "tashi mu je jikata,

Allah xae taya ni riko"

Bayan sun koma gida da kwana biyu inna ta fito cikin shirinta Rayyanat ma dake shirye cikin wani atamfa da aka dinko mata da hijab jiya tace "to Rayyanah jeki snr da hurera mu zamu fita."
Rayyanat ta nufi dakin hurera, dae dae nn Man ya shigo falon yana waya murmushi dauke a lebbansa, inna ta washe haqora tace "Allahu Akbar, sannu da xuwa d'an albarka dama kmr kasan neman wanda zai kaimu anguwar nake, sae gashi Allah ya jefo min kai"
Ya katse wayar da yake yana kallonta yace "kai Inna, ina xa ki cikin ranan nn" inna tace "yo ni rana da yana gasa mutum da bae gashe ni ba, kasan irin wahalar da na sha gidan mijina kuwa" ya tabe baki ya juya ya fita yace ina jiran ki a waje, tace "to to ynxu xa mu fito" tare inna suka fito da Rayyanah, yana jingine jikin motar yana jiranta don duk a tunaninsa ita da baaba hurera xa su fita, suna karaso gun motarsa ya zaro ido yana kallon innar yace "wae ke da wa xa ku fita?" Inna tace "yo Rayyanah mana" ya kuma xaro ido kmr wanda yaji abin tsoro cikin shan toka yace "nifa gasky baza ta shigar min mota ba, mgnr gskya knn, idan dai ke kad'ai ce to muje," inna ta tsuke fuska tana huci tace "yo naga ja'irin yaro, kai baka san tafiyar tata bace ma gaba daya, xuwa fa zanyi da it cikin dangi tasan kowa, kowa ya santa."

Girgixa kai yyi yana masu wani irin kallo yace "to ba da motata ba, ki kira Nasir da yyi maki hanyar ta ya kai ku" inna ta fashe da kuka tana girgixa kai tace "Ni ban san meyasa bn dace da jikoki ba a rayuwa duk sun rainani uwa ba ni na haifi ubansu ba" Muhammad ya girgixa kai yana kallon innar yace "bari to in kira wani ya kai ku inna kin ga fa sauri nake" inna ta hade rae tace "A'a sae dae ka kira ubanka Kabiru ya kai mu, idan ba shi ba kam al-quran bbu motar shegen da xan shiga" Muhd ya fuxa isa ya juya yana kallon Rayyanah yace "ke shiga muje" inna tayi murmushi tace "shiga Rayyanah" kasa shiga motar Rayyanah tayi fuskarta a daure, har sae da inna tace "ki shiga nace mana" snn ta shiga inna ma ta shiga motar tana goge dan kwallar idonta tana murmushi " sae da suka hau babban titi snn Muhd ya dake yace "ina muka nufa?" Inna tace "A'a wae da gidansu Murja xaka fara kai mu, daga can sae gidansu Fatee, daga gidansu fatee sae ka kai mu gidan bari'a,  daga can sae mu garxaya gidan kawata hjya Laure, in mun fito sae mu shiga gidansu Audi, to ba wani ddewa xa muyi a can ba, muna fitowa sae ka garxayo da mu gidansu Alhaji bukar, to daga gidan Alhaji bukar sae ka kai ni gidan tanko ina son gninsa, idan mun fito sae ka kai mu gidanku, daga gidanku kuma sae ka dawo da mu gida kawae don ni ban fiye son yawan gidajen mutane ba" murmushi kawae yyi yana shafa sajen fuskarsa bae ce mata komae ba.

Billy Giro😊
🔮🔮🔮🔮🔮🔮🔮🔮🔮🔮
[2:38PM, 5/2/2017] Billy giro😊: 🔮```BAZANBAR SHI BA!```🔮

```Na Billy giro😊```
```

26/12/2016

🔮```11```🔮
Sae da ya kaisu duk gidajen da inna ta lissafa snn ya kaisu gidan su wato family house.
6angaren hajiyar pretty suka fara zuwa snn 6angaren su hajiyar nasir wacce ta tarbe su cikin fara'a da murna ba kamar hajiyar pretty da ta kama kallon Rayyanat a yatsine ba.
Haka d'ayan 6angaren da girmamawa suka tarbi inna yayinda suke kallon Rayyanat ba yabo ba fallasa .

Nan inna tabar Rayyanat amma a 6angaren su hajiyar Nasir a cewar ta musu yini.
Saliha sai janta take a jiki sbd yarinyar tana da son mutane sosai ba kamar sauran yaran gidan ba hkn yasa Rayyanat ta d'an saki jikinta da saliha har ma tana jan Rayyanat da fira.
inda cikin firar take ta bata labarin rayuwar su ta school , ita dai Rayyanat saurarenta kawai take ba um ba um um sae dai idan taji abin dariya tayi d'an guntun murmushinta,saliha tace "wai nikam Rayyanat kin barni ni kad'ai keta zuba kamar parrot ba kuwa zan yarda ba don kema sae kin bani naki labarin makaranta,d'an guntun murmushi Rayyanat tayi snn tace"aini banyi secondary school ba ma bare zancen boarding school,xaro ido saliha tayi tace "hm kedai ba kya son bani labari ne,a sanyaye Rayyanat tace"da gaske nake wlh"
Saliha ta kalleta tace"meyasa gashi da alama zaki kai s .s 2 ko 3 inda kinci gaba?Baffana ne baya iya d'aukar nauyin karatuna"
tayi maganar cike da qwallah a idonta kan tuna baffanta da tayi"
Saliha tayi shiru tana kallonta sae duk taji ba dad'i tace"to ynx idan kika sami dama kina so kici gaba da karatun?girgiza kanta tayi tare da share hawayenta snn tace"ai lokaci ya qure min"
lokaci bai qure miki ba Rayyanat kina da lokaci har yanzu"
um um ynz ba wnn ne burina ba sae nn gaba kad'an tukun"er dariya saliha tayi tace"hm Rayyanat har wani buri kike da shi yanzu da ya wuce karatu sae dai idan karatun ne ba kya so"kallonta kawai Rayyanat tayi yayinda idanunta suka sake cikowa da qwallah ta kauda kanta gefe ba tare da tace da ita komai ba.
Qofa suka ga an turo saliha ta tashi taje ta kar6i trayn abinci da ke hannun ummnta ,hjy ta bata tare da kama kunnenta ta murd'e tace"kina nn kin cika ta da baqin surutun nn naki ko kiyi tunanin d'ebo muku abinci ma bakiyi ba, dariya saliha keyi mai had'e da jin ciwo tace"wash umma Allah inada niyyar tashi na d'ebo mana abinci sae gashi kin shigo mana dashi "ta sake mata kunnen tare da fad'in"oya yi ki zuba muku abincin kuci ina so zamu d'an fita ne zuwa anjima,to umma,nn Hajiya ta fita saliha ta zuba musu abinci a plate d'aya suka fara ci sae dai basu wani ci sosai ba Rayyanat tace ya isheta sbd dama kafin su fito taci abinci.

Sea bayan sllr la'asar suka fita wani qatoton mall suka je Hajiya tace da Rayyanat ta d'auki duk

abinda take so, Rayyanat bata iya d'aukar komai ba sae saliha ce ta shiga d'aukar mata kayan sawa kmr su Arabian gown da turarukku designers da kuma kayan kwalliya bayan sun gama siye siyen su ne suka maida Rayyanat gida da kayanta niqi niqi wad'anda saliha ta kwasar mata,
inna sae washe haqora take tana sama Hajiya albarka.

7 days later
Rayyanat ce a kitchen ta gama wanke kwanika tana goge kitchen bayan ta gama ta koma d'aki.
Saliha ce ta shigo gidan ta sami Mohd shida inna sae fira suke sae da ta gaishe su snn ta zauna har inna na tambayar ta ya mutanen gida tace duk suna lafiya tace"to ya na ganki yau ke kad'ai ba abokiyar yawonki Ameera? Tana gida wai yau bata jin fita tace"ayyo to ya hajiyarki tana lfy dai ko?lfiya qalau wlh ta ma ce a gaida ke,ina amsawa ai yau tama kirani a waya mun gaisa kmr kullum,eh inna Rayyanah fa? Shiga daga ciki yanzun nn ma ta shiga.
Rayyanat na zaune tana duba litattanfanta na islamiya sae ga saliha ta shigo da sallamarta ,da sakin fuska Rayyanat ta tarbe ta ta nemi guri ta zauna tare da jawo littafan Rayyanat na Islamiya tace"ke yau fa Alhamis ko kin manta" Rayyanat tace"ai ba shirin zuwa makaranta nake yiba ina muraji'a ne sae gashi na sami kaina da mantuwa da wani gun a cikin littafin ishmawee babun sallati janazatee gun da ake cewa....cab ai ke ban kai babin ba wlh kad'an dai ya rage,nn taja hannunta tare da fad'in "amma muje gun yaya Man ya tuna miki kafin ya fita "cikin rashin fahimta Rayyanat tace "waye kuma haka?oops baza ki san sunan ba sbd da Muhammadu inna ke kiran shi, Man kuma complete name d'inshi ne frnds d'insa suka had'e wato Muhammad Aminullah Nasir shine har mu qannansa ke kiransa dashi sbd koda muka taso mun samu ana kiransa da sunan.
Ta6e baki tayi ba tare da tace komai ba Saliha tace "muje ya tuna maki ko"um um nafi son na tuna da kaina sbd zanfi riqe abun da kyau"to amma dai zaki ajiye muraji'an nn har zuwa dare tukun sbd ina son muje ki rakani familyn mamana,a natse Rayyanat ta ware kyawawan idanuwanta tana kallon saliha snn tace"ni d'in nn? Eh man ai anguwar ba nisa da nn kuma wa ke kad'ai na biyo gidan nn wlh ,don hk ki tashi ki shirya mu tafi,nifa ban son shiga inda ban sani bane saliha ki tafi kawai abunki kinji,
,kinji Ki sae kace wacce za'a cinye dan Allah nidai tashi ki shirya mu tafi ai da sannu ake yin sabo ba wai zama zakiyi tayi kice ba kya shiga mutane ba.
Turo qofar da akayi ne ya katse Rayyanat da abinda tayi niyyar fad'a,Saliha tace"yauwa inna dan Allah ina son Rayyanat xata rakani gidan Baaba.
Ba musu inna ta amince da su tafi.
Duk da Rayyanat bata so ba amma haka ta haqura Saliha ta tasa ta gaba tana mata kwalliya yayinda tace ta rufe idonta har sae an gama kwalliyar ko zata bud'e,
byn an gama kwalliyar Rayyanat na bud'e idanuwanta ta wani ware su kan tsananin kyawon da taga tayi har ma ta fara shakkun anya ita ce kuwa tace"saliha wnn kwalliyar na tafi ina dashi nikam rage min ita don wlh ni ko kwalliya ma banayi bare na iya fita da wnn kwalliyar haka,,,um um gsky ba abinda zan rage maki ,
kawai don baki saba kwalliya bane kika ga kmr tayi yawa amma dai dai take, da qyar Rayyanat ta iya yarda aka bar kwalliyar saliha ta bata Arabian gown ta saka ta jawo qatoton hijabinta zata zuba saliha ta dalla mata harara da wasa tace"meye haka zan gani ki wani zuba hijabi har qasa

sae kace zaki tafi islamiyya ?ban gane ba saliha to dame kike son na fita?saliha bata ce mata komai ba sae hijabin ta cire mata ta d'auko top d'in gown ta roller mata, duk da cewa Rayyanat ba wata fara bace amma shirin ya matuqar d'aukar ta sae dai faffau tace bata iya fita da shirin sae tasa hijab Saliha ta buga qasa da sama a cewar ta duba ita ma fa irin shirin ne da ita amma ina sam Rayyanat bata yarda ba, bbu ynda Saliha ta iya da ita hka ta kyaleta da hijab din suka sallami inna da ke kitchen suna wainar flower da baaba hurera, inna na ganinsu ta washe baki tace "Ma'sha Allahu" saliha tace "ku fa ajiye mana namu inna, don nasan kina iya kwashewa gaba daya ki ba ma yaya" saliha na kai wa nn ta ja hannun Rayyanat suka fice daga kitchen din, kwance suka tar da shi a falo idonsa lumshe kmr mai bacci, Ikci daya ya bude ido yana kallonsu, Saliha ta dan hade rae tace "sae mun dawo yaya" Rayyanat kam kauda kai tayi ita ma fuskarta a daure, mikewa yyi xaune da sauri yace "ina xa ki?" Dauke kai tayi tace "gidan fa kaka xa mu, kuma Hajiya ta sani" kallon Rayyanat ya tsaya yi da mmki ganin ynda ta wani hade rae, can ya mike ya nufi kitchen sae ga shi ya fito inna na biye da shi a baya tana cewa "Ifya me ya faru?" Sae da suka karaso cikin falon snn ya juya yana kallon innar da kyau yace "dama tambaya ce xan maki, wae wnn yarinyar me aiki ce ko ko a ina kika jajubo ta" ya fadi yana nuna Rayyanat, inna ta ja dogon tsaki ta balla masa harara tace "uwar ka ce ba me aiki ba, wnn tayi maka kama da mai aiki, hka kawae kasa ma yarinya ido a gida, uwar me ta tsare maka, to in kai maye ne sae dae ka ci kanka wllh" a fusace ya karasa gaban Rayyanah yana mata wani mugun kallo fuskarsa a daure ya dago fuskarta da kyau yana kallo, ta kuma hade rae ita ma tana kallonsa da manyan idanuwanta, a nutse ya fara mgna, "daga yau, I mean daga this vry moment kika kuma min wani irin kallo a gidan nn, ko kuma kika gan ni kika ki gaida ni sae na....." Kukan da inna ta fashe da yasa ya tura ta da karfi, ya juya yana kallon innar, kwashe wayoyinsa yyi da ke kan kujera ya juya ya fice daga falon kmr xae tashi sama, inna ta bi sa da ja'irin yaro kawai, ta karaso gun Rayyanat tana matsar kwalla tace "kiyi hkuri kin ji 'yar nn, tambada yake ji yau shi yasa yyi maki hka, amma ki kyaleni da shi, da ubansa ma xan hada sa ni ya ja masa kunne ya daina xuwa min gida don baya tsinanani da komae da ma, sae dae in dafa in basa ya ci ya bar min kwanukan a nn ya kara gaba" Rayyanah tayi murmushi kawae tace "bbu komae inna" saliha da ko kadan bata ji ddin abinda yayan nata yyi ma Rayyanah ba ta ja ta a sanyaye suka fice daga falon don xuwa inda xa su.

Sae da suka fita daga gidan Saliha tace "kiyi hkuri Rayyanah hka yaya yake wani Ikcn" Rayyanah tayi murmushi tace "A'a ni bn ji haushi ba wllh," saliha tace "yauwa, kuma don Allah ki dinga gaishesa in kun hadu" Murmushi kawae Rayyanat tayi bata ce komae ba, saliha tace "ke komae murmushi, ba sae ki ce min to ba" Rayyanat ta kuma yi mata murmushin tace "toh naji Saliha" saliha tayi dariya tace "yauwa ko ke fa."

Billy giro😊
🔮🔮🔮🔮🔮🔮🔮🔮🔮🔮
[2:38PM, 5/2/2017] Billy giro😊: 🔮```BAZAN BARSHI BA!```🔮

```Na Billy giro😊```

28/12/2016

*🔮```12```🔮*
Washe gari  kaf gidan Rayyanat ce ta gyare shi har wajen gidan wato gun faka motoci duk sae da ta share tsaf koina  ya haskaka.
Snn taje kitchen don taya baaba hurera aikin abinci, baaba hurera tace "Aa Rayyanah yau kinyi aiki da yawa je kawai kiyi wanka kinsan yau juma'a qaramin lokaci ce," Rayyana tace "aa baaba bari kawai na tayaki wlh," "wlh jeki ai saura kad'an na qarasa tafi kiyi wanka kinji er albarka," cewar baaba hurera knn, murmushi kawai Rayyanat tayi ta juya ta fice daga kitchen. wanka ta je tayi ta shirya cikin riga da skirt na atamfa da inna tayi mata, sukayi mata kyau kmr ba tashin qauye ba kan yanda sukayi d'as a jikinta.
qur'ani ta d'auko ta shiga karatun suratul kahfi, a dakin da inna ta bata ita kadae duk da ba kwana take ciki ba don tsoro.

Tunda daga kan gate da mohd ya shigo gidan yake qare ma ko ina na gidan kallo ganin yanda gidan yayi haske yayi kyau, as in very neat ba wai don ba a share gurin ba a'a sae don ganin sharar yau ta daban ce da kullum.

Faka motar sa yayi ya fito cikin motar cike da tafiyar sa ta qasaita ya isa cikin gidan yana duba agogon wrist dinsa.
Inna ya samu xaune a falo ta miqe qafafu tana casbi har yana jin sautin salati na fita a bakinta, murmushi yyi hade da mata sallama, kin amsawa tayi sae ma wani kallon masifa da ta watsa mai tace "idan kasan yau ma tambad'ar ce ta kawo ka ftr min daga gida!"
Muhd yayi murmushi ya karaso cikin falon tare da ajiye ledar hannunsa gefenta yana kallonta yace "ni abinci naxo ci" inna bata kula sa ba sae hannu da takai tana bud'e ledojin da ya ajiye mata 'ya'yan fruits ne da gasasshen naman rago sae gassashiyar qullin hantar rago gefe, lkci daya inna ta washe baki tace "Auu! sannu da xuwa mai gida, Allahu yyi maka albarka ya kuma nuna min aurenka" daga haka ta qwalawa Rayyanah kira.
Cikin hanzari Rayyanat ta fito daga d'aki tana ganin muhd zaune ta rage saurin da take inna na washe da baki har lkcn tace "zo er albarka ki kai ma hurera 'ya'yan itacen nn ta yanyanka mana daga nn ki biyo ma maigidana da nasa abinci idan an kammala."
Rayyanah tace "to" ta kar6i ledar fruit wacce sae a snn ta gaida muhd, dake bin ta da harara tun shigowarta, ba yabo ba fallasa ya amsa.

Rayyanah ce ta yanka 'ya'yan fruits din da kanta ta had'o komai har da abincin mohd da inna tace, ta kawo ta ajiye ta wuce inna sae sa mata albarka take, inna ta dubi muhd washe da baki
```

har Ikcn  tace "d'an albarka nn ina son muyi wata magana da kai a game da yarinyar nn Rayyanah ashe wae primary kawai tayi sae jiya nake ji a bakin saliha shine nace ka binciko min makaranta mai kyau mai tsada kabiru ya biya a sata, in yaso duk safe sae ka riqa zowa kana kai min ita, Nasir kuma yana dawo da ita idan an tashi"
  Wani irin murmushi yayi da jin zancen inna kamar sa6o dan har ma sae da yayi istigifari a cikin rnsa had'e da shafo sajen fuskarsa yana kallonta har Ikcn murmushi dauke a lebbansa yace "to ynxu dae duk yawancin makarantu an fara jarabawan second term, kawae ki bari idan shekara ta zagayo hkn xae fi kyau" inna ta yi shiru tana kallonsa sae kuma tace "to muhammadu idan shekara ta zagayo dan Allah kar ka manta da zancen nn dan dai wlh ina son naga Rayyanah tayi karatu kmr kowa ga ta da kkri sosai in ji saliha"
 Yyi murmushi yace "to Allah kaimu" tace "amin" shi kuma ya jawo abinci ya fara ci.

2:30pm
Rayyanat ce zaune kan carpet ta gama sallah tana addu'o'i inna ta shigo d'akin kowane hannunta yana d'auke da plate d'ayan 'ya'yan itace ne da aka yanyanka, d'ayan plate din kuma naman rago ne da kuma hanta ta ajiye tana fad'in "Rayyanah keda nace kici abinci tun da'zu ashe baki ci ba sae yanzu da na fito naga komai inda na bar shi" Rayyanat tace "yanzu dama xan tashi idan na gama sallah" "to ai kin gama sllr tashi muje kici abinci a gaban ido na don na fhmci hlnki ba kya son cin abinci" ba yanda Rayyanat ta iya ta tashi tana linke sallaya had'e da d'an guntun murmushi a fuskarta don dai ita gsky tana jin dad'in yanda inna ke kula da ita.
  Falo suka je inna ta kunna musu kallo Rayyanah na cin abinci suna kallon su cike da nishad'i.

Washe gari ranr ta kasance ranr asabar Rayyanat tayi shirin ta tsaf na zuwa islamiya da hijabinta sky blue har qasa na islamiya ta saka safar ta klr hijabin ta d'auko niqab ta d'aura bata dai sake shi a fuskarta ta ba ta d'auko Jakarta ta islamiyya ta riqe a hannnu snn ta nufi d'akin inna ta mata sae ta dawo, inna tace "a dawo lafiya er albarka"
 Fuskar ta wasai ta fito d'akin ta saka takalmi ta rufe fuskarta da niqab snn ta fita, da kafa take xuwa makarantar don bbu wani nisa daga gidan can saman layi ne, yawanci duk gidajen masu da shi ne a layin don hka layin is vry cylnt, yau ma kmr kullum xaune ta gansa gaban kantamemen gate din gidan as usual, sae dae yau ba shi daya bne, shi da wani ne, bin ta yyi da kallo kmr ko da yaushe, ta wuce su da sauri tana harhardewa, ta rasa dalilin wnn kallon na mutumin nn da take gani kullum xata makaranta, ita dae fuskarta a rufe yake ko da yaushe, tsaki ta ja tana tunanin kila hanya kawae xata canxa don a rayuwarta ta tsani kallo.
Har aka tashi daga makaranta bata da wani walwala, ta hada litattafan da suka yi ranan ta xuba cikin jakarta snn ta sakale shi a hannu, ta dauki Qur'an dinta ta rungume a kirji ta sallami yan kawayenta da suka dan fara sabawa a ajin ta fito ta kama hanyar gida da sauri da sauri don Karfe shidda dama suke tashi, xaune ta sami mutumin daxu har Ikcn sae dae wnn karan shi kadae ne, tsallakawa tayi ta d'ayan side din ta ci gaba da tafiyarta da sauri, sae da ta dan yi nisa snn ta dan juya don ganin ko yana kallonta,Xuciyarta ya kusa shigewa cikinta ganin biyo ta ma yake, ta kara sauri gabanta na faduwa ssae, gashi bbu alamar mutum a layin, ganin duk saurinta har ya kusa cim mata yasa ta kwasa a guje ko minti biyar ba ayi ba ta isa gida har Ikcn gudu take har da kukanta, mai gadi na tambayarta me ya faru bata ko saurarsa ba ta nufi kofar shiga falo da gudu, a bakin kofa suka ci karo da Muhd dake tsaye yana jujjuya makulin motarsa

alamar xae tafi, suna mgna da inna, hkn yasa Rayyanat ta fasa ihu, ya koma baya da sauri Ikci daya ya turata da karfi ta fadi nn kasan falon, inna ta mike da sauri ta karaso bakin kofar tana salati tana tambayar me ya faru, Rayyanat da ke mayar da numfashi ta fashe da kuka ssae, inna duk ta rude ita ma ta saka kukan ta xube nn gabanta, baaba hurera ta fito da sauri tana tambayar Ifya, sae ga mai gadi shima ya taho da sauri yana tambayar me ya faru, Muhd kam don takaici komawa gefe yyi ya tsaya, cikin kuka inna ke kallon mai gadi da Baaba hurera tace "nima ban san kukan da take ba" baaba hurera ta shiga tambayar Rayyanat me ya faru, da kyar ta tsaida kukanta muryarta na rawa tace "wani mutumi ne sae yyi ta kallona idan xa ni makaranta, shine yau ya biyo ni sae na fara gudu yana ta bi na kuma" ta karashe mgnr cikin matsanancin kuka, juyawa Muhd yyi ya fice daga falon mai gadi ya bi bayansa, Ikci daya inna ta tsuke fuska ta miqe tana share hawayen fuskarta tana huci tace "dan gidan uban waye shi xae biyo min ke da gudu, hurera dauko min gyale na" hurera tace "A'a inna, ba ga su Muhammadu sun fita ba" inna tace "da'alla bani mayafina in je in masa rashin mutunci" hurera ta dauko mata gyalenta ta bata, ta fixge ta fice daga falon kmr xata tashi sama, a bakin gate suka hadu da Muhd da mai gadi, Muhd yace "ina xa ki kuma inna" ba tare da ta kallesa ba tace "nemo dan iskan xan je yi mana" yace "bbu kowa a waje na duba, ita bakauyiyar wace gari ce da xata d'aga ma mutane hankali hka, kila ma harkan gabansa kawae yake xata shigo ta daga ma mutanen gida hnkli, tsiyar yan kauyen nn knn"

Billy giro😊
🔮🔮🔮🔮🔮🔮🔮🔮🔮🔮
[2:38PM, 5/2/2017] Billy giro😊: 🔮```BAZAN BARSHI BA!```🔮

```Na Billy giro😊```

30/12/2016

🔮```13```🔮
Cikin gida suka koma tunda ba a ga wanda ake neman ba, inna dai sae masifa take tayi kmr wacce ta sami wanda ake nema a gabanta.

Mohd kan takaici tun daga kan gate bai ma dawo ba jan motar sa kawai yayi yabar gidan.
Inna ta rarrashi Rayyanat ta samu har ta daina kukan da take taje d'akinta ta ajiye jakarta ta cire niqab da hijab da socks ta nemi guri xata kwanta sbd har yanxu jikinta bai daina rawar tsoro ba.
Inna ce ta shigo d'akin riqe da kofin fura a hannunta,
ba ita tabar d'akin ba har sae da Rayyanat ta shanye furar tas.
```

Har dare Rayyanat bata sake kmr kullum ba kallo suke amma sae tunanin gobe take idan zata je islamiya.

Nasir ne ya shigo gidan da sallamar sa ,suna gama gaisawa inna ta bashi Ibrn abinda ya faru da Rayyanat d'azun ,
ya kalli Rayyanah da kulawa yace"bai dai maki komai ba ko? Sae da ta girgiza kanta snn tace"bai min komai ba amma nasan ko gobe zan ganshi in na fita don kullum sae na ganshi idan zan tafi makaranta"
ta qarashe mgnr kmr wacce zata yi kuka.

Nasir ya nisa yace har da safe kike ganin sa idan zaki tafi makaranta? Aa bana ganinsa da safe sae da yamma"

To shikenan da yamma zanzo kiyi tafiyar ki kar ki nuna tsoron komai don so nake na gane dalilin bibiyarki da yake,kar kisa tsoro dmn ina nn a bayanki kinji,a sanyaye ta gyad'a masa kai . Inna tace"ai kowane d'an iskan ne gobe ma kwashe ta nida shi"

Nasir yace"ai ba girmanki bane inna ki barni dashi kawai"...yo shi girma ya sani ne da zai biyo er qaramar yarinya haka duk yabi ya tayar mata da hnkli gabad'aya yau ta rasa sukuni.

Ai inna ina ganin irin en iskan samarin nn ne da basa da abinyi sae zaman banxa.

Inna ta tsuke fuska tace"to Rayyanah kam baza tayi komai dashi ba don ya ma kama gabansa tun wuri.

Nasir yayi murmushi ya sauya wata firar suka ci gaba dayi,
can inna ke tambayar sa wai ina er banzar nn Fatima ta shige da na daina jin d'uriyar ta, Nasir ya shafi kansa yana murmushi snn yace"inna ai pretty ta jima bata jin dad'i sbd laulayin da take fama dashi"

Dad'i inna taji sosai har da su taka rawa ta kusa samun kama kunne tace"ai bari shi kuma d'an banzan nn yazo marar son aure ,yazo yayi auren nn ko shima zanga abinda ya haifa kafin nabar duniya.

Duk cikin taka rawa inna ke maganar nn Rayyanat har da er dariyar ta don rawar inna ta bata dariya sosai.

Washe gari da yamma har Rayyanat taje ta dawo bata had'u da kowa ba,
tare suka shigo ita da Nasir inna na ganin su ta shiga tambayar ko anga mutumin ?Nasir yace"ba muga kowa ba sae wasu masu zama gurin"
wani dogon tsaki muhd dake kishingid'e yaja yace"wai inna me yasa kike biyewa bagidajiyar yarinyar nn nikam,kawai mutane na harkar gaban su ta wani ce ya biyota in miji take nema taje can qauyen su mana ta samo irinta ba tazo nn tana fakewa da wani ya biyota ba,
wane kidahumi ma zata samu a nn da har zai yi lokacin ta in ba wanda uwar sa ta masa baki ba.

Sosai maganar mohd tayi wa Rayyanat baqiqirin a rai duk yanda taso 6oye hawayenta sae da suka gangaro kan kumatunta tayi saurin share hawayen ta shige daga ciki ,mohd dake kallonta cikin 6acin rai sae a snn ya kauda idonsa ya maida su gun inna da ta shiga sirfa mai masifa kan yafita harkar Rayyanah har tana fad'in "sae na had'a ka da ubanka kabiru idan baka fita

harkarta ba wlh.
Nasir ne ya shiga bata haquri shida baaba hurera dake aiki kitchen ta jiyo fad'an ta fito" mohd kam barin gidan yayi sai haushin inna yake ji dake fifita Rayyanah akan shi har tana sako ubansa a ciki.

Yau kusan kwana biyu mohd bai zo gidan inna ba inna bata damu ba sai ma harkar gabanta take.

Rayyanah ce a bayan gida ta gama wankin kayanta dana inna tana shanya wacce sae ta sharce zannuwan kafin take shanyawa.

inna tazo ta same ta tace"oh ni wai Rayyanah wanki kika xo kina mana keda ya kamata ace kinyi shirin islamiya !uhm inna ai na kammala yanzu zanje in shirya "to Rayyanah yi maza amma dan Allah ki daina wankin nn nasha gaya maki akwai mai min wanki har ma naki d'in duk ki daina wankewa idan sun taru ki kawo na had'a da nawa kayan na bawa abu mai wanki ya riqa wanke mana kinji.
Rayyanat ta gyad'a mata kai inna ta washe baki snn tace"to yayi er albarka yi maza ki shirya ki tafi makaranta.

Tafe take cike da fargaba don har yanzu bata cire ran zata sake ganin wanda ke bibiyar ta ba gashi yanxu nasir yayi tafiya bare ya rakota kmr yanda yayi mata a kwana biyun nn da suka wuce.
Sai sauri take har tana hard'e qafafu jin alamar ana binta a baya dmn har sautin tafiya tana ji , kan tsananin tsoro bata iya juyawa ba sae ma duqawa tayi zata kwashi takalmanta ta banka da gudu.
Sae taji an mata sallama cikin murya mai mugun taushi da sanya natsuwa ga duk wanda yaji hkn yasa ta fasa abinda tayi niyya sae dai cike da 6acin rai ta miqe dmn ganin wanda ke neman takurata a rayuwa.

Billy giro😊
🔮🔮🔮🔮🔮🔮🔮🔮🔮🔮
[2:38PM, 5/2/2017] Billy giro😊: 🔮```BAZAN BARSHI BA!```🔮

```Na Billy giro😊```
```

30/12/2016

🔮```14```🔮
Murmushi ya sakar mata duk da ba ganin fuskar tata yake ba kansancewar niqab d'inda ke sanye da ita.
Kafin ya ce komai ta buga mai uban tsaki tace"wai malam lfy kake faman bibiyar rayuwata!wani murmushi ya sake sakar mata yakai hannu cike da natsuwa ya shafo sumar kanshi snn yace"sbd ina sonki"harara ta dallah mai had'e da tsaki "ta tafi ta barshi nn tsaye,
Bai bita ba sae tsayuwar sa ya gyara tare da hard'e hannuwan sa a qirji yana kallonta har ta 6ace ma ganin sa.
Juyowar da zaiyi ne sukayi ido hud'u da Man dake masa wani mugun kallo na tsana yace"kai amma ka bani kunya wlh kai yanxu baka ga abin bibiya ba sae wnn abar "uhm man kenan wnn ce abar yrnyr da ta koina ta amsa kiran mace har mace ga natsuwa da kamala .....mtsw! Man yaja tsaki yace"ga dukkan alama ka fara shaye shaye shiyasa kake ganin abu baibai,nn ya tafi ya barshi kmr wanda zai tashi sama.
Gidan inna ya nufa ya sami inna da baaba hurera zaune a tsakiyar gidan suna fira.
Ya gaida su sae baaba hurera kad'ai ce ta amsa gaisuwar ,
inna dake hararamsa ganin zai shigar mata d'aki tace"me kuma zakayi min a cikin d'aki bayan duk gamu nn a waje"baaba hurera tace"ke ko dai inna mai gida ne fa ai kya tashi ku shiga ciki kiji dame yazo,
ai nasan ba abinda yazo dashi face tambad'a da iya shege,ni kwana biyun nn ma da baka zo ba sae naji sat kmr an cire min qaya.

Kujerar zaman mata naga man ya jawo wacce su inna ke zaune kan irinta yasa farin handkerchief d'insa ya share snn ya zauna yana fuskantar inna d'auke da murmushi a fuskar sa yace"ashe inna in na mutu kin huta dani kenan... zaro ido tayi tace"me kuma ya kawo zancen mutuwa ana zaune qalau, to inna ke kika ce kinji dad'i da banzo kwana biyun nn ba, yo dan nace haka Muhammadu ai bazan yi ftr ka mutu ba nida nake son ganin 'ya'yanka kafin na bar duniya tukuna ma wai kai don ubanka yaushe zakayi auren ne kullum kana mana yawo da hnkli baka ko son ana zancen,
ni ka gaya min idan kana fama da rashin lafiya ne inji dan insan ta inda zan fara nemar ma magani, sajen fuskar sa ya shafo yana kallon inna wanda har lokacin da murmushi d'auke a fuskar sa yace"inna me kuka dafa yau? Ban sani ba ina ma magana kana wani zancen, oh ni Hajara wai ko dai muhamnadu gamo kayi da aljana da duk ana ma zancen aure sae ka canza da wata maganar,ta qarashe mgnr cikin kuka irin na tsafi d'in nn, mohd ya kalle ta da kulawa yace"nifa inna kinsan na tsani na ganki kina kuka indai aure ne nayi kusa nn bada jimawa ba inshaAllah"
Kai zo kuka farin ciki gun inna har da su rawa tana yiwa man kari kan irin farin cikin da yasa ta yau ta jashi zuwa d'aki sae zuba
masa albarka take yayinda baaba hurera tabi su da kallo tana dariya dn har lokacin inna rawa take man kuwa sae murmushi yake don shi yana son ko yaushe yaga inna cikin farin ciki .

Inna da kanta taje ta kawo mai abinci wacce yinin rnr duk cikin farin ciki tayi shi.

6:5pm
Rayyanat ce ta shigo gidan ta dawo daga makaranta ta sami man kwance a falo kan 3 seater kmr mai bacci don idanuwan sa a rufe suke, tsaye tayi tare da yaye niqab d'in fuskar ta tana masa kallo mai cike da tsana,
karaf idanuwansu suka had'u tayi saurin kauda idonta tare da gaishe shi ba tare da ta damu da ya amsa ko kar ya amsa ba tayi ficewar ta zuwa d'akinta.
Da sauri man ya tashi ya bita ya finciko hannunta da qarfin tsiya har sae da jikinsu ya had'u sae kuma yayi saurin ture ta daga jikin nashi ya nuna ta da yatsa yana fad'in"ba nayi warning d'inki kan wnn d'an iskan kallon da kike min ba ,wlh ina mai gaya miki duk na qara kama ki kina min irin wnn kallon na lafira sae yafi ki jin d'adi!dan ubanki inni sa'anki ne ko kuma abokin wasarki!
Zama d'aya qwalla ta ciko a idon Rayyanah kan jin zafin zagin da ya mata,ta d'ago tana kallonsa haka shima kallonta yake har hawaye suka fara sakkowa a hnkli kan kumatunta .
Ya watsa mata mugun kallo snn ya bar d'akin Rayyanah kuwa share hawayenta tayi snn ta ajiye jakar hannunta ta cire hijab da socks ta kai su a muhallinsu.
Tayi zamanta a d'aki har sae da ta tabbatar mohd ya bar gidan snn ta fito taje d'akin inna wacce tana ganinta ta washe baki tana tarbon ta da murna kyace ta kwana bata ganta bane.

Bayan sati d'aya da faruwar haka Mohd ne zaune a office d'insa yana waya kan cewa "a bashi ixini ya shigo"ya ajiye wyr ba jimawa aka turo qofa ya kafe wanda ya shigo da ido har ya zauna.
Hannu suka bawa juna suka gaisa snn wanda ya shigo ke cewa"Man magana naxo muyi mai muhimmanci kuma dan Allah kar kayi poking d'ina"man dake jingine ya lumshe ido tare da sauke ajiyar zuciya snn yace"ina jinka"
Kallon sa yayi da kyau yace"about wnn yarinyar ne da nake bibiya idan zata tafi islamiya ashe ma ka santa"da sauri man ya bud'e idonsa dake rufe yace"aka ce maka na santa who say so? Nop ba wanda yace kawai ni naga hkn sbd a kullum gidan inna nake ganin tana shiga haka kuma gidan take fitowa"to ban santa ba nima ganinta kawai nake a gidan"
A sanyaye mutumin yace"to naji ganin ta kawai kake da haka nake so ka taimaka min kamin jagora muje ko yrnyr nn zata fara kulani dmn wlh nayi nayi ta kulani taqi gashi ni kuma dgske nake sonta wlh"
Man da tunda ya fara zancen sa yake masa kallon ka ta6u yaja dogon tsaki tare da girgiza kansa yace"tabbas munir ynx na tabbatar ka fara shaye shaye amma ka 6ata kanka wlh ka kuma cuci iyayenka da tarbiyar da suka maka"
Cikin damuwa munir yace"wai Man meye hk duk a cikin frnds kafi kowa sanin halina fa....banda yanzu da ka sauya halayen ka don haka ni ka ma ftr min daga office,pls man.... Munir!nace ka fita ko!
Cikin 6acin rai munir ya tashi ya fita ya bar mohd dake juyi a hnkli kan kujerarsa yaja guntun tsaki yace"na rasa wace irin qwaya ce yake sha dake sauya mai tunani gabad'aya da har ya

fad'a jin son wnn abar har ma wai yake cewa na masa jagora sae kace ni d'an makauniya ne ko makaho"

Billy giro😊
🔮🔮🔮🔮🔮🔮🔮🔮🔮🔮
[2:38PM, 5/2/2017] Billy giro😊: 🔮```BAZAN BARSHI BA!```🔮

```Na Billy giro😊```

1/1/2017

🔮```15```🔮
Munir yaro ne kyakkyawa mai matuqar mutunci da kamala haka kuma yaro ne mai girmama manyansa ya kasance mai tausayin talakawa sosai sbd haka ya taso ya sami iyayen shi da son taimakon talakawa duk da irin kud'in sa kuwa basa da wulaqanci ko kad'an asali ma gidan su munir gida ne da ko yaushe zaka sami jama'a wad'anda ake bawa taimako.
Su biyar ne a gun iyayen su ,shine na farko snn hameed ,Hasheem,Hafsat snn er autar su safiyya.
Munir ya jima yana son yayi aure amma bai sami wacce ta kwanta mai a rai ba sae akan Rayyanat wacce ko da kuskure bai ta6a ganin fuskarta ba amma rnr farko da ya fara ganin ta yaji ta kwanta mai a rai ya kuma ji a ransa irin matar da yake son aura ce.

Ranar alhamis ba islamiya hakan yasa Rayyanat tayi zaune tana ta mitar littafanta,
ita kad'ai ce a falon tana karantawa da larabci tana fassarawa tamkar tana a gaban malami yanda ta taqarqare.
Ba komai yasa taxo falo tana yin karatun ba sae don inna ta fita anguwa baaba hurera kuma tana kitchen,gashi inna tace xa'a kawo saqo shiyasa taxo falo ta zauna kar wanda inna tace zai zo ya kawo saqo yazo basu ji ba.
Rayyanah yarinya ce mai tattara hnklinta gabad'aya akan abinda ta sa ma gaba hkn yasa bata san da shigowar Mohd ba duk da kuwa sallamar da yayi sae ganin mutum kawai tayi tsaye a kanta, a tsorace ta saki ihu tare da jefar da littafanda ke hannunta zata kwasa da gudu kenan man ya dakatar da ita cikin daka mata tsawa, sae kawai ta fashe masa da kuka tana kallon shi ,wacce sae a snn ta gane waye,ai kuwa kai tsaye ta had'e girar sama da ta qasa tare
```

da share hawayen fuskarta, Mohd kuwa tsaki yaja yayi tsaye yana kallonta yayinda hannyen sa ke cikin aljihun wandonsa,ciki ciki ta gaida shi ta duqa ta kwashi littafan ta ta wuce ta kaisu d'akinta ta ajiye snn ta nufi kitchen dai dai baaba hurera ta shigo ta qofar baya duk a rud'e, tace"Rayyanah ba kece naji ihun ki ba ina bayi?

Kmr wata qaramar yarinya ta 6ata fuskarta tace"nice Baaba wnn d'in nn ne ya shigo ban sani ba sae ganin sa nayi shine na tsorata"

Baaba hurera tace"waye kuma wnn d'in nn ?Rayyanah tace"wnn d'in nn dake zuwa gun inna kullum.

Baaba hurare kam bata gane ba sae falo ta tafi dan ganewa idonta ,
tana ganin mohd ta washe baki snn tace"ayyo wai muhammadu kaine Rayyanah ke cewa wnn d'in nn sae duk ban gane ba shine nace bara na fito naga waye.

Murmushi ya sakar mata tare da gaida ta snn yace"inna fa na shiga d'akin nata ban same ta ba"

Baaba hurera da har lokacin murmushi take tace"ai ta d'an fita ne ita da Nasiru amma tace bazata jima ba zata duba Fatima (pretty) ne dake jin jiki,to Baaba ace da wnn yrnyr ta kawo min abinci na,Baaba hurera tace "to"snn ta koma kitchen ta snr da Rayyanat.

Tun daga qofar kitchen mohd ya tsare Rayyanat da mugun kallo har ta qaraso ta ajiye masa abinci zata juya yace"ke xo nn"

Juyowa tayi tare da watsa masa manyan idanuwanta a cikin nashi,
guntun tsaki yayi ya kauda nashi idanun sae kuma ya sake kallonta snn yace"wae ke wace ce da kika raina ni haka meye matsalar ki dani?kauda idonta kawai tayi ba tare da tace dashi komai ba, ya saki tsaki yace"tafi ki bani guri amma wlh duk rnr da na qara jin kince min wnn d'in nn sae bakin ki ya gaya miki"

Ta juyo had'e da ta6e baki ta fara tako kenan taji yo sallama ta amsa sallamar ta tafi ta kar6o saqo ,
kitchen ta tafi da saqon dan inna ta gaya mata abinda za'a kawo wato nmn kaji,tas Rayyanat ta wanke nmn ta zuba a freezer.

Washe gari rnr juma'a Rayyanat taci er kwalliyarta ta juma'a tana zaune abinta a d'aki ta gama karatun srtl kahfi ta jawo litattafanta na islamiya tana mita.

Tana cikin haka taji inna na qwala mata kira ta fito da sauri taje falo ta sami inna dasu saliha da Ameera nn ta saki fuska suka gaisa  da saliha akasin Ameera da ta qi ko kallon gefen Rayyanat.

Inna ta kalli Rayyanat washe da baki tace"dama yanzu nake shirin kiranki kixo kici abinci sae ga su saliha sun shigo kinga sae kije ki d'ebo maku abincin kuci tare"

Rayyanat taje ta d'ebo masu abinci a  qaton plate ,
fried rice ce da akayita ta da qoda tayi kyau sosai har ta gaji d'auke da paper chicken  da aka d'ora a gefe.

A nn falon sukayi zaune zasu ci ,
saliha ta kalli Ameera wacce ta maida hnkli kan TV bata da niyyar tasowa suci abinci

,tace"Ameera taso muci abinci ke muke jira fa"da d'an mamaki Ameera ta kalli saliha snn ta nuna kanta da yatsa tace"ni d'in nn'sae kuma ta wani  yamutse fuska tana kallon Rayyanat kmr wata abar qyama tace"kuci kawai ni a qoshe nake sae dai zuwa anjima ko zanci"kafin saliha tace komai inna tace"kinga bana son iya shege tashi kuje kici cikin taro ai yafi"
  Wlh inna a qoshe nake sae dai zuwa anjima,ke kika sani cewar saliha wacce tuni ta fhmci dalilin da yasa Ameera taqi tasowa suci abincin.
  Suna cikin cin abinci saliha ke cewa "yauwa Ameera idan mun qarasa cin abinci ina son muje ki rakani gidan su yaya munir gun safiyya na kar6o house wears d'ina sbd dai dai su nake son amin sabbin da za'a d'inka min"
  Ameera tace"to gama d'in muje ko banza ina son naje naga safiyya"
 Wlh kam safiyya nada qoqarin ziyartarmu"cewar saliha wacce ta kalli Rayyanat tace"tare fa zamuje dan ki hanzarta cin abinci naga sae ci kike kmr ba kya so"Rayyanat tayi murmushi tace"to so kike ina cin abinci sauri sauri naje har ya sarqe ni ai komai sannu a hnkli yafi"
  Murmushi saliha tayi tana mai kallon Rayyanat tace"hakane amma kin fiye shiririta gun cin abincin naki in nice ma sae ya girshe ni kafin na qoshi, shiyasa nake sauri abuna sae na kammala cin abincin ina mai marmarin sa don nafi son haka,kema idan kika gwada yin haka zaki fi jin dad'i.
    A sanyaye Rayyanat ta kalli saliha tace"har abada bana son sauya tsarin cin abinci na sbd haka na taso na sami Abbana yana ciyadda ni.
  Tana kawowa nn hawaye suka sakko kan kumatun ta tayi saurin tashi ta bar gurin yayinda saliha ta bita da ido cike da tausayi.
  Ameera ta ta6e baki tace"kukan name kuma ana zaune qalau? Ajiyar zuciya saliha ta sauke tace"bari kawai Ameera wlh Rayyanat abin tausayi ce dmn ta bani labarin rayuwarta ciki har da mutuwar mahaifinta da shi kad'ai ne gatan ta a duniya kinga dole tayi kuka a duk lokacin da ta tuna shi,Ameera ta wani  ta6e baki tace" to Allah ji qan mamata"
  Amin cewar saliha wacce ta tashi taje ta lallaso Rayyanat ta shiryo suka fito .
  Ameera kam ganin da Rayyanat za a tafi tace ta fasa bata zuwa su dai gaida safiyya, ko kad'an saliha bata damu ba duk da ta fhmci dalilinta.
  Inna suka je sukayiwa sallama suka fita ta bisu da Allah  dawo daku lafiya.

Gidan ba nisa sosai dan qasa ma suka bi ,suna shiga gidan Rayyanat ta tsaya ta kasa shiga ba don komai ba sae don hango munir da tayi zai shiga mota,
 sosai gabanta ya fad'i don ta rasa wane irin mutum ne shi da duk inda taje sae ta had'u dashi.
  Saliha ce ta riqo hannunta tana fad'in"zo muje mana"
  Haka Rayyanat ta dake tabi saliha sbd tasan idan ba gamo tayi ba ba zai gane taba tunda kullum cikin niqab yake ganinta.
  Da sauri ta sadda kanta qasa ganin irin kallon da yake mata har ma ya fasa shiga mota ya nufo su yazo ya tsaya gab da ita,gam ta qara riqe saliha dmn ta gama yarda gamo tayi, saliha kuwa sae washe baki tayi tana kallon munir tace"yaya munir ina wuni? Fuskar sa wasai ya amsa mata har yana tmbyr ya su umma tace"duk suna lafiya.

nn taja Rayyanah zasu wuce, yayi saurin dakatar da ita kan cewa "ki shiga kawai qawar ki zata same ki daga baya"

da qyar saliha ta iya qwace hannunta daga na Rayyanat ta tafi ta barsu d'auke da murmushi a fuskarta.
 Da hanzari Rayyanat ke qoqarin bin saliha munir yayi saurin shan gabanta yace"yau kam ba inda zaki sae kin saurareni"
 Kuka kawai ta fashe masa dashi dan gabad'aya ta gama tsorata dashi.

Billy giro😊
🔮🔮🔮🔮🔮🔮🔮🔮🔮🔮
[2:38PM, 5/2/2017] Billy giro😊: 🔮```BAZAN BARSHI BA!```🔮

```Na Billy giro😊```

2/1/2017

🔮```16```🔮
 Cikin muryar sa mai saka natsuwa ya shiga bata haquri har ta tsagaita kukanta da takeyi marar sauti.
 Cikin kulawa ya kalleta da kyau snn yace"kin tsorata dani ko shiyasa kike kuka,ko kad'an baki da laifi a bisa tsoratar da kikayi sbd ban ta6a ganin fuskar ki ba amma yau ina ganin ki na gane kece ,
 kin san sbd me na gane ki?
 D'agowa tayi tana kallon shi ,
Shi kuma kmr wanda ke tsaye da er shekara shida yace"to yi min magana man sae na gaya miki"
 A sanyaye tace"sae ka fad'a"
 Murmushi yayi tare da nuna gefen zuciyar sa yace"ta nn na gane kece sbd duk lokacinda na gnki zaki tafi islamiyya bugun xuciyata ya kan canxa har sae kin 6acewa gani na,shiyasa nake tunanin idan na rasa ki ya zanyi dmn nasan zuciyata zata iya lalacewa ta bar jikina,da haka nake roqon ki kan dan Allah ki amince dani kinji.
 Kallon sa tayi shaye da toka tace"kaga malam ni zan shiga ciki"
 Sosai ya langwa6ar da kansa cike da son kora mata wani bayani tayi saurin girgiza kanta alamar bazata saurare shi ba ta kuma kama hnya ta bar gidan sae kiranta yake yana rarrashi kan ta dawo ya shigar da ita cikin gida amma fafau taqi tsayawa.

Tana isa gida dai dai ta kai tsakiyar falo sae kawai taji ta fashe da kukan da ta rasa dalilinsa ai
```

kuwa da gudu ta shige d'akinta don bata son wani  yaga tana kuka,sbd sam hnklinta bai bata ganin kowa a falon ba alhali kuwa Mohd da Ameera suna nn zaune.
  Ameera ta kalli mohd da ya tsure qofar Rayyanat da kallo kmr mai wani  nazari can ya maida duban sa ga Amira yace"ita wnn daga ina ta fito? ta6e baki tayi snn tace"gidan su yaya munir ta raka saliha ,saurin kallonta yayi jin gidan da ta ambata ita kuma ta qarasa da cewa"wata qil qauyanci  ta nuna musu shiyasa suka koro ta"
  Komai bai ce mata ba sae tashi yayi ya fita.

Rayyanat na cikin kukanta taji an turo qofa tayi saurin tashi ta share hawayenta ,saliha wacce ta shigo taxo gab da ita ta zauna ta riqo hannyenta cikin murya mai kama da ta rarrashi tace"haba Rayyanat meyasa kike ma yaya munir haka yace tsawon lokaci yake bibiyarki amma kinqi ki saurare shi,don Allah Rayyanat ki taimaki yaya munir wlh na fhmci mugun sonki yake ,Hawaye ne suka gangaro kan kumatun Rayyanat tace"saliha ki bawa yayanki haquri dmn tunda yaya anwar ya mutu na ajiye soyayya ba kuma zan qara ba ko banza ma bazan iya soyayya da mutumin birni ba ,meyasa zaki ce haka Rayyanat naga ko yaya anwar a labarin ki da kika bani shi d'an birni ne,eh amma shi asalinsa d'an qauyen mu ne nace maki ba tashin birni bane ,amma Rayyanat d'an birni da na qauya ai duk abu d'aya ne dmn duk Allah ya yisu'"um um ba d'aya bane saliha,akan me zaki ce haka? Sbd ba d'aya bane,ajiyar zuciya saliha ta sauke tana mai kallon Rayyanat tace"indai hali kike tunani to wlh yaya munir yana da halin kirki....a zahiri ba dmn baki san meye bad'inin sa ba"
